# ZABI
# MAI MULKIN
## ZUCIYARKA



WANENE KA KE SO
YA ZAUNA A ZUCIYAR KA

# ALLAH KO IBLIS?

AMSARKA ZAI SA KA INDA ZA
KA YI RAYUWARKA NA HAR ABADA

# KA TABA SON WANI SOSAI?

## KO MACE, KO NAMIJI, KO YARO KO UWA, KO UBA, KO ABOKI?

Saanan, za ka sani cewa kana da zuciya - za ka ji soyayya mai zurfi a ciki. A wasu lokatai za ka ji kiyayya a wurin, ko fushi, ko kishi. Allah yana so mu kaunace shi da dukkan zuciyar mu. Koyaushe yana bincike zuciyarmu.

Kodayake Iblis yana son zuciyar-ka kuma -- domin ya mallake ta ya kai ka ga hallaka.

**ABIN DA ALLAH YAKE BA KA:**
Idan za ka gaskanta shi don ya cece ka, da kuma ka yarda ka juyo daga zunubanka, kuma ka karbe yafewarsa ta wurin Dansa Yesu, Allah yana so ka zama abokinsa. Kuma zai ba ka kyantar rai madawami. Zai mallaki zuciyarka ta wurin Ruhunsa. Zai kuma kare ka daga mugunta ya kuma albarkace ka yayin da ka gaskanta da shi.




**ABIN DA IBLIS YAKE BA KA:**
Rayuwar zunubi a yanzu. Amma nan gaba, ka kasance da shi har abada a wani wuri da ake kira jahannama. Wata rana Iblis tare da wadanda suke bauta masa, za a jefa su cikin jahannama. Iblis da masu binsa za su sha wahala matuka har abada abadin, duk da haka ba za su mutu ba.

Mutane ba za su shiga jahannama ba don mummuna ayyukarsu ba (mai lakabi zunubi) wanda sun aikata a rayuwarsu, amma don sun ki da ganaganci yafewa da Allah ya ba su da kuma sun ki shi Ya zama abokin su da Mai Ceton su.
Ina son yi maka tambaya mai tsanani.

## WANENE KE MALAKAR ZUCIYARKA A YANZU HAKA?

## ALLAH KO IBLIS?

Ka duba wannan hoton zuchiyar mutumin nan. Watakila zai taya ka gani gaskiyan. Iblis yana tsakiya kuma ba shi kadai ba ne. Dabbobi a nan danan alamu ne kawai. Alamu na mummuna halayen a zuciyar mutumin nan.

Ka duba wannan hoton zuchiyar mutumin nan. Watakila zai taya ka gani gaskiyan. Iblis yana tsakiya kuma ba shi kadai ba ne. Dabbobi a nan danan alamu ne kawai. Alamu na mummuna halayen a zuciyar mutumin nan.
Akwai sauran zunabai shaawa da fasikanci (bunsuru), shaawar kazanta (alade), maita (kunkuru), kiyaya da fushi (damisa) kishi (maciji) da hadama (kwado). Lamirin mutumin nan (tauraro) ta yi duhu.



Idon yana gaya mana cewa Allah yana duba zuciyar mutum. [1Sam 16:7]. Ya san zurfin asirai na kowane mutum. Ayanzu haka Allah yana ganin kome da kome na zuciyarka…babu abin da za ka boye masa.



## ALLAH YANA KAUNAR KA!

Yana so ya cece ka daga zunubanka da kuma daga tarkon Iblis mai ban tsoro. Amma kafin Allah ya cece ka, wani mutum da farko sai da ya biya don zunuban ka.
Sai da aka hori wani mutum ya sadauka da ransa a maimaikon ka kafin Allah ya yafe zunubanka.

Wan can mutumin shi ne Yesu, Dan Allah. Saboda Yesu Dan Allah, Koyaushe Yana nan, Mai Tsarki, Nagari kuma cikkake, amma Ya yarda Ya shigo duniya daga sama ya zama hadaya don zunubanka. Ya mutu sabili da kai domin ka karbi yafewa, ka zama aboki da Ubansa.

### Ka ga hoton?

Wannan ne abin da Yesu Ya yi maka Ya mutu ta wurin buga shi cikin hanaye da kafafu a kan giciye kuma ta hanyar nan Ya zama laanane don Ya dauka laanar daga wurin ka har abada. Jini ya zuba yayin da Ya mutu wannan jinin kadai zai iya wanke zuciyzar ka daga zunubi kuma ya kare ka daga mugunta.
Allah yana da babbar kauna ma ka. Yana so ya fid da zunubi da Ibilis daga zuciyarka da rayuwarka. Yana so ka juya wurinsa, ka gaskanta da shi ya cece ka.


## KA YI AMINCI!

Ka yi amince kuma ka yarda cewa ka yi zunubi kuma ka na bukatar kauna da yafewa wanda Allah Yana ba ka.

Sai ka roki gafara daga wurin Allah. Yana son ya gafarta maka saboda Yesu Ya zama hadaya domin zunubanka.

Ga addua mara wuya da za ka yi;

*"Ubangiji Allah, na yi zunubi. Yanzu da na ga hoton nan, na gane da gaskiya ni mai zunubi ne. Ibilis yana mulki na kuma yana so ya hallaka ni. Ina rokonka, Ka gafarta zunubai na ka kuma dauke Ibilis da zunubi daga zuciyata da rayuwata yanzu. Ka aika Danka, Yesu, da kuma Ruhunka Mai Tsarki cikin zuciyata don ya cece ni kuma Ya kare ni daga mugunta. Zaka iya yin wannan saboda ka fi karfin Ibilis. Kai kadai ne Allah na gaskiya. Kai ne Allah Mai iko duka. Ina so daga yau Ka zama Allah na".*




**Ka yi wancan adduar?**

Littafin Allah, Littafi Mai Tsarki, ya ce idan mun furta zunubanmu, Shi mai alkawali ne, mai adalcii kuma, da za shi gafarta maka zunubanka, shi tsarkake ka daga dukan rashin adalci.

# BABBAR MUSAYA

Ka ga wannan hoto- kurciya-Ruhu Mai Tsarki yana nan, ka roki Allah ya cika zuciyar ka da Ruhunsa mai salama kuma ya zuba maka albarkunsa.

A musayar zunubanka Allah ya ba ka alherinsa, [adalci] na Dansa Yesu. Adalci yana nufin mai gaskiya wurin Allah (wato ka na da alherin Yesu a zuciyarka) kuma yana ganin ka cikakke ne a cikin Yesu. Yanzu zaka iya shiga haikalinsa mai tsarki.



Ka zama aboki da Allah saada an gafarta maka zunubanka kuma ka karbi wannan kyautar adalcinsa. Lokacin da ka karbi gafartawar Allah ta wurin gaskanta cewa Yesu ya mutu sabili da kai, ka zama sabon mutum.

Saboda adalcin Yesu a kan ka (wadda aka wakilta da hoto na ginshiki) an




gayyace ka cikin ainihin haikali Allah (Ibraniyawa 10:16)

Za ka iya Magana da shi kai tsaye kuma kada ka bukaci wani ya yi Magana a maimakonka. Ruhun Allah zai taimake ka.

Samun shigar haikalin Allah kamar haka da bangaskiya, zai canza zuciyarka da tunaninka. (Ezekiel 36:25-27) Sa'anan duk abubuwan da ka ke yi za su fara canzawa zuwa mafi kyau. Wannan irin saduwa na mutum da kansu da Allah an wakilce shi da tsania a hoton.

Wadansu mutani suna ki su sami irin wannan abokantaka da Allah. Zakaran da ke hoton alamar wancan musu ne

Zai kuma cece ka a kuma kare ka daga ikokin Ibilis da na jahannama.

Wannan hoto yana nuna abin da ke faruwa a yamzu.

Hasken Allah yana haskaka kuma Ibilis da zunubi suna kaucewa ko fita waje! Ruhun Allah na nuna shi da hoton kurciya wadda yake kawo haske cikin zuciyar ka a yanzu, saboda Allah haske ne.

Ka roki makiyayi (Pastor) ya bayyana maka baftisma kuma a shirya maka rana baftisma. Baftisma yana Magana a kan mutuwa game da rayuwar ka na da da kuma sabuwar rayuwa a cikin Yesu.

## KATIN BA DA AMSA

Cika wannan sashe YANZU kuma ka aika zuwa a direshin nan na kasa:

**Na Zabi Yesu ya yi mulki a zuciyata da rayuwata!**

Suna na ______________________________

______________________________

Adireshi na ______________________________

______________________________

Kaba da wannan kasha zuwa:

Every Home

**Every Home for Christ Nigeria**
(North East)
Flat 8A, Close E, Wole Soyinka Federal Roads Safety Estate, Kuchikau 1 Karu Local Govt. Nasarawa State.
GSM: 07062020396, 08069169411